# Ya Allah ina roƙon Ka dukkan alheri, magaggaucinsa da majinkircinsa, abin da na sani daga gare shi da abin da ban sani ba, kuma ina neman tsarinKa daga dukkan sharri magaggaucinsa da majinkircinsa, abin da na sani daga gare shi da abin da ban sani ba

Daga (Nana) A'isha Uwar muminai - Allah Ya yarda da ita - cewa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya koya mata wannan addu'ar: "Ya Allah ina roƙon Ka dukkan alheri, magaggaucinsa da majinkircinsa, abin da na sani daga gare shi da abin da ban sani ba, kuma ina neman tsarinKa daga dukkan sharri magaggaucinsa da majinkircinsa, abin da na sani daga gare shi da abin da ban sani ba. Ya Allah ina roƙonKa mafi alherin abin da bawanKa kuma AnnabinKa ya roƙeKa, kuma ina neman tsarinKa daga sharrin abin da bawanKa kuma AnnabinKa ya nemi tsarin Ka da shi, ya Allah ina roƙonKa aljanna da abin da yake kusantota na magana ko aiki, kuma ina neman tsarinKa daga wuta, da abin da yake kusantota na magana ko aiki, ina rokonKa Ka sanya dukkan hukuncin da Ka hukunta gare ni ya zama alheri".

[Ingantacce ne]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya koyawa Nana A'isha - Allah Ya yarda da ita - dunkulallun addu'o'i su ne addu'o'i huɗu: Na farko: Addu'a mai game kowane alheri: (Ya Allah ina roƙonKa dukkan alheri) dukkansa, (magaggaucinsa) makusanci a lokacinsa, (da majinkircinsa) na nesa, (abinda na sani daga gare shi) daga abinda Ka sanar da ni, (da abinda ban sani ba), daga abinda yake kasancewa a cikin saninKa - tsarki ya tabbatar maKa - . A cikinsa akwai fawwala al'amari zuwa ga Allah Masani Mai bada labari Mai sawwaƙawa; sai tsarki ya tabbatar maSa Ya zaɓawa musulmi maffificinsa kuma mafi kyansa, (Ina neman tsarinKa) ina neman tsarinKa ina kiyayewa (da Kai daga sharri dukkansa magaggaucinsa da majinkircinsa, abinda na sani da abinda ban sani ba). Addu'a ta biyu: Ita ce kiyayewar musulmi daga ya yi shisshigi a cikin addu'a (Ya Allah lallai ni ina roƙonKa) ina nemanKa (daga mafificin abinda bawanKa kuma AnnabinKa ya roƙeKa) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi, (ina neman tsarin Ka) ina fakewa ina nenam tsari (da Kai daga sharrin abinda bawanKa kuma AnnabinKa ya nemi tsarin Ka) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi , wannan addu'a ce da nema daga Allah Ya bawa mai addu'ar daga abinda Annabi Muhammad - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya roƙe shi kuma ya neme shi ga kansa, ba tare da ƙididdiga nau'ikan abinda tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - da shi ya roka ba. Addu'a ta uku: Neman shiga aljanna da nisantar wuta, shi abin neman kowane musulmi ne kuma matuƙar aikinsa: (Ya Allah ina roƙon Ka aljanna) da rabauta da ita (da abinda ya

kusantota na magana ko aiki) na gari wanda zai yardar da kai, (ina neman tsarinKa daga wuta) inda babu tsari daga munanan ayyuka sai da luɗufinKa, (da abinda ya kusanto zuwa gareta na magana ko aiki) daga saɓon da zai sa fushinKa. Addu'a ta huɗu: Addu'a da yarda da hukuncin Allah (ina roƙonKa Ka sanya kowane hukuncin da Ka hukunta mini ya zama alheri) dukkan al'amarin da Allah Ya hukunta shi gareni Ya sanya shi mafi alheri gare ni, wannan yana daga addu'a da yarda da hukuncin Allah.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/5487

النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY

لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee